# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: ’Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na shida: Riba nan, zafi can

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Dije: | ’yar shekara 19 |
| Amina: | ’yar shekara 19 |
| Dorathy: | ’yar shekara 18 |
| Direba: | ɗan shekara 30 |
| Duduwa: | ’yar shekara 35 |
| Mandu: | ɗan shekara 40 |
| Fasto: | ɗan shekara 40 |
| John: | ɗan shekara 25 |
| Jane: | ’yar shekara 24 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, lalle marhabin da sake kasancewa da ku a cikin kashi na shida na shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan mutane masu fama da taɓin hankali a nahiyarmu ta Afirka. A cikin shirin da ya gabata, kun ji yadda Duduwa ta ci bashin kuɗi wajen mai maganin gargajiyan nan Maude don ta yi kuɗin mota zuwa birni inda za ta kai Musa ta nema mishi magani. Kun dai ji yadda maƙwabtanta suka ƙona mata gida saboda wai suna zargin cewa mayya ce. A wani wurin kuma, daga ƙarshe dai John ya yarda ya bi fasto waje don su ɗan zagaya bayan matarshi ta haihu. Kuma a kan hanyarta ta komawa gida tare da ƙawarta Dorathy, Dije kwatsam sai ta ga ƙawarta Amina wadda ta ɓace. Tana zaune a kan titi ko kaya babu a jikinta. To daga nan, ina muka dosa?

Ku biyo mu cikin shirin namu na yau mai taken "Riba nan, zafi can". Kuma za mu faro labarin ne daga inda muka tsaya, wato daga irin ruɗanin da Dije da Dorathy suka shiga a lokacin da suka ga Amina da tsakiyar dare.

**Fitowa ta 1: A hanya**

**Dije:** Me zan gani haka! Lallai Amina ce waccan, me ya same ta? Yaya aka yi ba kaya a jikinta, kuma duk ta yi datti, sannan kuma tana cikin sanyi a kan titin nan mai hatsari da daddare? Dorathy, ya kamata mu taimake ta.

**Dorathy:** Mu taimake ta? Ke ma ba kya cikin hankalinki ne? Dije, ƙawarki ta haukace, ba za ki iya taimakon ta ba. Idan da ana iya taimakonta, da ba za mu riƙa ganin duk mahaukatan da muke gani ba a kan titi ba. Kin ga, ki zo mu yi tafiyarmu kawai, mu ƙyale ta, saboda dare na ƙara yi.

**Dije:** A'a, ba zan iya tafiya in bar ta ba! Bai kamata a ce Amina na cikin sanyin nan ba, sam bai kamata ba. Ba dai haka ba.

Ai sai mugayen 'yan daban nan su yi amfani da halin da take ciki su ci zarafinta, kuma …

**Dorathy:** Haka ne, na sani Dije. Za a iya yi mata fyaɗe, amma kuma ai haka masu zama a kan titi suka gada. Haka abubuwan suke. Don Allah ki zo mu tafi, ko ma samu mu yi barci. Kin san fa gobe muna da *class*.

**Dije:** Ki je kawai, ni zan ga abin da zan iya yi. Amma don Allah ki taimaka min da gyalen nan naki saboda mu rufe mata jiki.

**Dorathy:** Ki manta kawai! Gyalena ba na rufe wa mahaukaciya jiki ba ne. Wannan gyalen fa kyauta ce ta musamman aka yi min. Yi haƙuri, ni ba zan iya ba ki ba.

**Dije:** Dorathy, ina ce a matsayinmu na masu koyon aikin nas, kamata ya yi mu fara kawo tunanin taimakon wanda ba shi da lafiya tukuna kafin komai. Amina na buƙatar taimakonmu.

**Dorathy:** Amina na buƙatar taimakonki dai! Ni kin ga tafiyata. Sai gobe, sai mun haɗu.

**Dije:** Amina. Kin gane ni?

**Amina:** Dije? Ina jin sanyi. Sanyi na damuna sosai.

**Dije:** Kin gane ni? Yaya aka yi haka? Me ya sami kayanki, Meena? Ina kika shige tuntuni? Zo mu bar wurin nan.

**Amina:** Dije, ina jin yunwa. Yunwa na damuna sosai.

**Dije:** Wannan wane irin abu ne haka! Ga shi kina magana sai ka ce mai hankali! Amma kuma ga shi kina nan. Sa wannan rigar sanyin, na san ba za ta isa ba amma dai za ta kai mu gida.

**Mai ba da labari:**
Taɓin hankali wani abu ne mai wahalar ganewa kuma mai sarƙaƙiya. Hatta ƙwararru a kan taɓin hankali kan sha wahala a kan ba da bayanin abin da ya jawo shi. Kuma kamar yadda muka gani a wajen Amina, taɓin hankali ba ya hana waɗanda suke fama da shi su riƙa gane mutane, ko tuna wani abu, ko kuma su rasa tunaninsu gaba ɗaya. Sai Dije ta yi ƙoƙari ta rufe wa Amina jikinta, sannan ta kama hannayenta suka tafi wajen shiga mota.

**Dije:** Amina zo mu shiga wannan. Ba kowa a ciki saboda haka muna iya zama a baya.

**Direba:** Ke, ke! Ina za ku shiga? Sauka! Sauka daga motar nan na ce. Ba ma ɗaukar mahaukata.

**Dije:** Mene? Ba ka da hankali ne? Kake cewa mu mahaukata ne? Ka san abin da yake fitowa daga bakinka. Kuma muna da ikon shiga motar nan. Kawara ba ta da lafiya, kuma gida zan kai ta.

**Direba:** Kin ga, Malama. Na ce miki mu ba ma ɗaukan fasinjoji mahaukata. Ku kira motar ɗaukar marasa lafiya mana ko kuma ku yi shatar tasi. Ku fita yanzun nan daga motar nan!

**Dije:** Wannan ba daidai ba ne. Bari in yi magana da direban!

**Direba:** Kin ga ni ne direban, kuma ni ne karen motar, kuma kin san wani abu? Motar ma tawa ce. Saboda haka kar ki ɓata lokacina da naki, ku fita ku nemi wata motar.

**Dije:** To shi ke nan, zan biya kuɗin kujerun bayan. Mu je. Kawata tana jin yunwa kuma sanyi na damunta.

**Direba:** Ni ba ni da sha'awar kuɗinki, ko ba ki gane ba ne? Ni ina so ne ku fita a motata kawai! Kin gane ko? Duba abin da kuka janyo mini, duba! Dubi yadda sauran fasinjojin ke shiga wasu motocin saboda ku! Sannan ga shi motata ta fara wari. Mts! Don Allah ku fita.

**Dije:** Yi haƙuri Amina, zo mu fita.

**Amina:** Ga su nan zuwa za su tafi da ni! A'a, ni ba zan tafi ba!!

**Dije:** Amina don Allah! Kar ki fara don Allah. Ki fito kawai mu tafi! Za mu san yadda za mu yi mu je gida. Kin ji?

**Amina:** Don Allah kar ku tafi da ni. Kar ku tafi da ƙawata Dije.

**Dije:** Amina, ba wanda zai tafi da mu ko'ina. Ina nan tare da ke. Tashi mu tafi!

**Amina:** Ba zan iya tsayawa a nan ba, za su ɗauke ni.

**Dije:** Don Allah ka taimake ni ka tsai da min da ita! Tana so ta gudu ne. Don Allah, ka tare min ita!

**Direba:** Mene? Ba zai yiwu ba!

**Dije:** Amina, don Allah ki tsaya!

**Direba:** Kai, yau fa ba kanta. A’a. Mahaukata biyu suna bin juna a guje. Gaskiya ba mu da sa’ar fitowa yau.

**Mai ba da labari:**
Abin takaici, sai ka ga mutane sun mai da masu taɓin hankali kamar dabbobi. Kamar jama’a su yarda da cewa ne, masu taɓin hankali mutane ne amma ba ruwansu da kowa. Dije sai ta yi ta bin Amina da gudu, a yayin da ita kuma Aminan tana ta gudu ne daga mutane da muryoyin da ita kaɗai ta ke jinsu. Wanshekare a dai wannan garin Duduwa ta iso tare da ɗanta Musa, bayan tafiya mai tsawo da suka yi zuwa birnin. Yanzu ga ta nan a ƙofar gidan yayanta Mandu.

**Fitowa ta 2: A gidan Mandu**

**Mandu:** Wane ne?

**Duduwa:** Yaya Mandu, ni ce Duduwa.

**Mandu:** A’a, Duduwa ke ce? Me ya kawo ki garin nan haka? Musa, kai ne ka yi girma haka!

**Duduwa:** Mu shigo ne? Duk a gajiye muke wallahi.

**Mandu:** Kwarai kuwa, ku shigo. Ku zauna! Musa, zauna a nan kusa da bango. Me zan kawo muku?

**Duduwa:** Yunwa muke ji sosai. Saboda haka muna buƙatar abin da za mu ci. Amma kafin nan, akwai labarin da nake so in faɗa maka.

**Mandu:** A'a, kai Musa! Ka daina buga kanka a bangon nan haka. Duduwa, ki ce mai ya daina! Maƙwabtanmu za su yi magana.

**Duduwa:** Kar ka damu, za su saba. Za mu ɗan daɗe da kai in dai ba za ka damu ba.

**Mandu:** Mene? Za ku ɗan daɗe? A ina?

**Duduwa:** Da kai mana, yaya Mandu. Kai ne fa kaɗai ɗan'uwan da nake da shi a duniyar nan, ina kake so in je? Kar ka damu kanka da Musa, ina ganin sai na ƙara ɗaure shi ma, amma ba yanzu ba.

**Mandu:** Uhmm… Duduwa… Ina ganin wannan ba shawara ba ce mai kyau. Bayan wannan ma, to wa zai riƙa kula miki da wurinki a ƙauye a yayin da kike nan?

**Duduwa:** Yaya Mandu ke nan! Ba ni da wani wuri. An ƙona min gidan jinkana. Za mu iya samun wani abu mu sha kuwa?

**Mandu:** An ƙona miki gida! Duduwa, me kike faɗi ne haka? Ba wani abu da yake damunki? Ko ke ma za ki …

**Duduwa:** Ba in da zan tafi. Mun zo mu zauna a nan ne har sai an ƙara gina min gidana. Don Allah, ba wani abin da za mu sha? Tun da muka taho Musa bai ci komai ba.

**Mandu:** Abin da na so in tambaye ki shi ne cewa ko ke ma kin fara hauka ne? Ga ruwan ku sha.

**Duduwa:** Maƙwabtana ne suka ƙona min gidana. Wai suna tunanin cewa ni mayya ce kuma ta dalilina ne Musa ba shi da lafiya, wai kuma ni ne na sa bala'o'i ke faruwa a ƙauyen.

**Mandu:** Wannan wane irin hauka ne! To ke me ya same ki, yaya aka yi da ke da Musa kuka kuɓuta?

**Duduwa:** Yaya Mandu, labari ne mai tsawo. Amma yanzu dai ina so in ji. Za mu iya zama a nan ko kuwa?

**Mandu:** Ah ... ina ganin za ku iya … amma na 'yan kwanaki kawai. Sannan kuma kar ki bari a ga Musa! Ban ba kowa labarinshi ba.

**Duduwa:** Haka ya yi daidai. Sai dai akwai wani abu ɗaya, ina da niyyar in kai shi ya ga ƙwararren likita a babban asibiti. Saboda haka za mu tafi gobe da sassafe.

**Mandu:** Kai Musa, me kake yi kuma haka, kana ta shirya jaridu a wuri ɗaya? Za ka gina ɗakin ajiye jaridu ne?

**Duduwa:** Haka yake yi ko a gida ma da itacen girki.

**Mai ba da labari:**
A ko da yaushe, taɓin hankali da Musa yake fama da shi, yakan sa shi ne ya riƙa shirya abubuwa a wuri ɗaya. Amma mene ne sunan irin wannan yanayin? Nan ba da daɗewa ba za mu ji amsar. Amma yanzu bari mu koma gidan John. Ciwon takaici ne yake damunshi, kuma yanzun nan ya dawo daga wani zagayen shaƙatawa da suka fita da shi da fastonshi.

**Fitowa ta 3: A gidan John**

**Fasto:** Kai John, gaskiya na ji daɗin zagayen nan da muka yi.

**Jane:** Wai! Na ji daɗi da na gan ku. Har kuna dawo? Da har na fara tunanin… To kun yi magana a kan abin?

**John:** A'a, a gaskiya ba mu ce wa juna komai ba a wannan zagawar da muka yi. Amma dai na ji daɗin kukan tsuntsaye da kuma ganin yadda shuke-shuke ke kaɗawa. Har ma na fara mantawa da kyan halittun nan da kuma irin baiwar da Allah ya yi mana.

**Mai gabatarwa:**

Da haka kuma muka kammala shirin na yau. Sai kuma shiri na gaba idan Allah ya kai mu. To me ya faru a wajen? Haka na nufin cewa John ya fita daga ƙangin takaicin da yake fama da shi? Me zai faru da Duduwa da ɗanta Musa a birni? Sannan kuma Dije za ta ƙara gano Amina kuwa? Duk za ku ji waɗannan a shiri na gaba idan Allah ya kai mu. Kafin nan kuna iya tuntuɓarmu a adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraron wannan shirin: dw.de/lbe. Kuna iya haɗewa da mu a shafinmu na Facebook domin yin muhawara ko aikawa da sakwanni. Ku huta lafiya. Sai mun haɗu a shiri na gaba.